Na kasance ina wanka ni da Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - daga kwarya (abin wanka) daya mu duka biyun muna da janaba, ya kasance yana umartata, sai insa gwafso, sai ya rungumeni alhali ni ina al’ada,

Daga Nana Aisha Uwar Muminai - Allah Ya yarda da ita - ta ce : Na kasance ina wanka ni da Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - daga kwarya (abin wanka) daya mu duka biyun muna da janaba, ya kasance yana umartata, sai insa gwafso, sai ya rungumeni alhali ni ina al’ada, ya kasance yana fito min da kansa alhali shi yana i'itikafi sai in wanke masa shi alhali ina al’ada.

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Nana A'isha uwar muminai - Allah Ya yarda da ita - ta bada labari game da sashin halayenta na musamman tare da shi tsira da amincin Allah su tabbata agare shi, daga hakan: Ta kasance tana wankan janaba tare da shi tsira da amincin Allah su tabbata agare shi- daga kwarya daya sai su dinga diban ruwan tare. Kuma cewa shi tsira da amincin Allah su tabbata agare shi idan ya yi nufin zuwa mata alhali tana al’ada sai ya umarceta ta rufe jikinta daga cibiya zuwa gwiwa, sai ya rungumeta da abinda ke koma bayan jima'i. Kuma cewa shi tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya kasance yana i'itikafi a cikin masallaci sai ya fitar da kansa ga Nana A'isha alhali tana cikin dakinta tana al’ada.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/3476